# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na bakwai: A wurin bautar Ubangiji

Wanda ya rubuta: Romie Singh
Wanda ya tace: Katrin Ogunsade, Naïma Guira
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja

**'Yan Wasa:**

Dauda: ɗan shekara 17
Layla: 'yar shekara 16
Maryam: 'yar shekara 16
Rabaran Haruna Emah: ɗan shekara 40
Malam Isma'ila: ɗan shekara 43, baban Layla
Nas Rakiya: 'yar shekara 28
Hassan: ɗan shekara 12, ɗan'uwan Layla
Tafida: ɗan shekara 17

**MAI GABATARWA:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na bakwai daga cikin goma na wasan kwaikwayonmu na shirin "Ji Ka Karu" a kan "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka haddasa zaman doya da man ja tsakanin wasu al'ummomi guda biyu da kuma gidaje biyu. To sai in ce ku biyo mu domin jin yadda shirin nan na yau zai kasance mai taken "Wurin bautar Ubangiji".

An sami ƙanen Layla, wato Hassan, da hannu dumu-dumu a cinna wutar da aka yi a wani coci a garin Sodangi, wanda yake ƙarƙashin ikon Fada Bana. Ba shakka, burin da ƙungiyar Musulmi take yi na ta gina sabon masallaci a wani fitaccen wuri a cikin garin Sodangi ya sami cikas. Ga dukkan alamu, Hukumar Raya Birane ta wannan gari za ta ba wa Fada Bana goyon baya ga gina coci a wannan fili. Haka dai ya faɗa wa Malam Magaji, wanda shi ne babban editan nan na jaridar "Muryar Jama'ar Sodangi". Dangantaka tsakanin Kiristoci da Musulmi ba ta taɓa tsami ba kamar a wannan lokacin. A kowace rana ta Allah idan an tashi daga makaranta, sai Dauda da Layla sun gana a ƙarƙashin gadar Sodangi. Duk lokacin da suka tattauna a kan abin da zumunta ke nufi, to sai ƙauna ta ƙaru tsakaninsu. Za ku kuma ji ko Hassan, ƙanen Layla wanda ya sami rauni, ya canza tunaninsa a kan ma'aikaciyar jiyyar nan, wato Bayahudiyar nan mai suna Rakiya?

**Fitowa ta 1: A ƙarƙashin gadar Sodangi**

Tafida, Dauda, Layla

**DAUDA:** Layla, abar ƙaunata, ni da ke mun zama ɗaya.

**LAYLA:** Kama hannuna, Dauda!

**MAI BA DA LABARI:**

Kamar yadda ruwan kogin Sodangin nan mai ƙasa-ƙasa ke kwarara, haka Tafida ya yi imanin cewa idan har yana da muradin jan hankalin Layla, to ya zamanto dole ya kafa wa Dauda tarko. Idan kuwa haka ne, sai ya yi amfani da

Maryam, yarinyar nan da ta tsaya a matsayin Layla a Kungiyar Muhawara ta makarantarsu domin ita ma tana ƙaunar Dauda!

**Fitowa ta 2: A Cocin 'Yan Majami'ar Bautar Ubangiji Mai 'Yanci**
Maryam, Dauda, Rabaran Haruna Emah

**MARYAM:** Ya ko Dauda! Da ma ina so in gayyace ka don ka je ka gane wa idonka yadda mu 'Yan Majami'ar Bautar Ubangiji Mai 'Yanci muke bikin addininmu. Zo mu tafi don har Rabaran Haruna Emah ya fara wa'azi.

**DAUDA:** Wai wai wai! Ke Maryam, waccan haɗaɗɗiyar motar tasa ce?

**MARYAM:** E, masu zuwa cocinsa ne suka saya masa ita. Ni ma sai da na ba da gudummawa, kuma ina jin daɗi duk lokacin da na tuna cewa, har da gudummawata aka haɗa aka sayi motar.

**DAUDA:** To amma fa ni duk talakawa na ga suna zuwa cocin. Me suke da shi balle har su bayar da wata gudummawa?

**MARYAM:** Ɗari da kwabo, haka suke bayarwa. Shi Rabaran Haruna mai ceto ne fa. Kai ma ka shiga ko ka sami ceto, don kuwa zai iya cetonmu duka.

**RABARAN:** Ku matso, ku matso! Kowa ya sami albarka, *hallelujah!*

**JAMA'A:** *Hallelujah!*

**RABARAN:** Ubangiji na tare da ku, *hallelujah!* So muke mu tara dala dubu biyar. Dala dubu biyar don aikin Ubangiji. Ubangiji shi ne zai saka wa masu miƙawa, *hallelujah!*

**MARYAM:** Ka ga, bari na sa ma wannan a wuyanka Dauda. Wannan wata alama ce ta cewa akwai Ubangiji guda ɗaya da ake bauta wa.

**DAUDA:** Mene ne?

**MARYAM:** Wani kuros ɗin gwal ne.

**DAUDA:** Amma ai ba zan....ba ma sa wata alama ta addini a makaranta.

**MARYAM:** Kai don Allah can, ba a makaranta kake ba, a wurin bautar Ubangiji kake.

**DAUDA:** Kin ga, ina jin bai kamata Rabaran Haruna Emah ɗin nan naku ya ɗauki kansa a matsayin wani wanda ya san gaibu ba, ko kuma ya riƙa raba talakawa da kuɗinsu. Duk ya jefa su cikin wani irin hali. Kalle su fa ki gani!

**MARYAM:** Ai Ruhu Mai Tsarki ne ya shige su.

**DAUDA:** Kai ba wani Ruhu Mai Tsarki. Kurun dai ana yaudararsu ne ana karɓe musu kuɗi, wanda kuma hakan ba daidai ba ne. Ai mutumin da yake aikin Ubangiji bai kamata ya raba talakawa da kuɗinsu ba, kamata ma ya yi ya ba su.

**MARYAM:** Mu Ubangiji muke bautawa a tamu cocin, muna bayarwa ne don raɓin kanmu.

**DAUDA:** To, ni zan tafi. Sai mun haɗu ranar Litinin a makaranta**.**

**MAI BA DA LABARI:**

To a halin yanzu kuma, Layla tana son ta yi wa babanta magana a kan halin da Hassan yake ciki saboda har yanzu ba ya yarda ya ci abinci ko ya sha maganin da wata nas Bayahudiya take ba shi a asibiti. Wannan bai sa Nas Rakiya ta yi watsi da shi ba, amma ita Layla, abin yana damunta sosai. Ran nan sai ta yi sa'a baban nasu ya dawo gida da yamma. A wannan daren shi ne ma ya dafa musu abinci mai daɗi, ga shi kuma ta fahimci yana cikin yanayin da zai iya sauraronta.

**Fitowa ta 3: A gidan su Malam Isma'ila**

Layla, Malam Isma'ila

**LAYLA:** Na gode Baba. Wannan irin abinci mai daɗi haka, ga lemo. Sai ƙanshi ne ke tashi! To amma fa Baba, da ma ina son in yi magana da kai a kan Hassan. Ko ka san har yanzu ya ƙi yarda da duk wani taimakon da Nas Rakiya take ƙoƙarin yi masa, saboda shi a ganinsa, wai ita ma irin mutanen nan ce da yake kira "ma'abota littafi".

**MAL. ISMA'ILA:** To sai me in Nas Rakiya Bayahudiya ce? In ba don ita ba ai da yanzu babu shi! Kin ji shi ko! Ko waye ke cusa masa irin wannan ra'ayin? Mu ba ma kafirta abokan arzikinmu waɗanda ba Musulmi ba.

**LAYLA:** Shekarunsa sha biyu fa kacal, Baba. Zai iya daina irin waɗannan halayen, za a kuma iya nuna masa yadda zai zama mutumim kirki a rayuwa. Amma sai mun ƙara kusantarsa fa, Baba. Tun lokacin da Mama ta mutu, in ka lura za ka ga yana janye jikinsa daga mutane. Ina jin waɗannan ɗaliban na makarantar Islamiyyar nan, su suka cusa masa wannan ra'ayi.

**MAL. ISMA'ILA:** To yanzu me kike son na yi, Layla?

**LAYLA:** Kamar yadda na faɗa, Baba, dole ne ni da kai mu ƙara kusantarsa. Haka kuma sai mun sa ido a kan abin da yake yi, da kuma irin abubuwan da yake karantawa. Duk yaron da ake lura da shi ba zai ƙona coci ba, Baba! Nas Rakiya mutuniyar kirki ce, kuma ina ganin tana son ta taimaka.

**Fitowa ta 4: A asibiti**

Nas Rakiya, Hassan

**NAS RAKIYA:** Hassan, don Allah ba ni hannunka na gwada bugun jininka. Haba na wajena.

**HASSAN:** Ni ba na so na zama na wajenki.

**NAS RAKIYA:** Ka ga Hassan, ni nas ce, zan iya taimaka maka ka sami sauƙi. … 80 bisa 120. Yauwa! Bugun jininka yanzu ya yi daidai. Ka ga, manufar halittar ɗan Adam a bayan ƙasa ita ce ya aikata alheri. Na san addininka ya faɗa maka haka, ni ma nawa addinin haka. Zan iya aikata alheri ta hanyar taimakonka.

**HASSAN:** An faɗa min Yahudawa kafirai ne.

**NAS RAKIYA:** Hassan, dukkaninmu nan Allah ne ya halicce mu, kuma ya rage naka ka yi imani da abin da ka ga ya fi dacewa. Amma in har ko da yaushe za ka ce za ka riƙa kallon bambance-bambance da ke tsakanin mutane maimakon ka kalle su a matsayinsu na 'yan Adam, to ko da yaushe zaka riƙa zama cikin ɓacin rai.

**HASSAN:** Ke Bayahudiya ce, ba kya ƙaunar Musulmi.

**NAS RAKIYA:** Wannan ba gaskiya ba ce! Addinina ya koyar da ni cewa Musulmi da Yahudawa Allah ɗaya suke bautawa, kuma dukkaninmu zuriyar Annabi Ibrahim ne. Birnin Kudus ƙasa ce mai tsarki a wurinmu gaba ɗaya. Dukkaninmu daga tsatso ɗaya muka fito. Mu 'ya'yan Annabi Adam ne fa, Hassan.

**HASSAN:** Ni kawai, so nake na mutu na tarar da babata.

**NAS RAKIYA:** Hassan, na yi imani Allah ne za busa mana rai. Rayuwarka tana da muhimmanci, bai kamata ka salwantar da ita ba. Ka duba Alƙur'ani mai tsarki littafin da aka saukar wa Musulmi, ka karanta ayar da ta ce: "Kada ku kashe kawunanku. Haƙiƙa Allah shi ne ma fi jin-ƙai gare ku".

**HASSAN:** Ni ban cancanci jin-ƙai ba.

**NAS RAKIYA:** Ka cancanci ka samu mana! Dole ne ka daure ka manta da kome! *Rayuwa tana faruwa, …*

**HASSAN:** Nas Rakiya, ina da ciwo a hannayena. Don Allah za ki iya taimaka min na sami sauƙi?

**NAS RAKIYA:** Mu gani! … Bari in shafa maka wannan man! Yauwa!

**HASSAN:** Wash! Wayyo! … Kai! Har na ji dama-dama.

**NAS RAKIYA:** Madalla! To, ka kwanta ko ka samu ka ɗan runtsa.

**HASSAN:** Na gode, Nas Rakiya.

**MAI BA DA LABARI:**

A can kuwa makaranta, tunanin da Tafida yake yi na kafa wa Dauda tarko, sai ya ɗauki wani sabon salo, lokacin da Maryam ta sami Tafida a ɗakin karatu.

**Fitowa ta 5: A ɗakin karatu**

Maryam, Tafida

**MARYAM:** Tafida, Tafida! Dauda ya sa kuros a wuyansa.

**TAFIDA:** Ke! Garin yaya Maryam?

**MARYAM:** Ni ce na ba shi jiya. Na san ya manta ma yana wuyansa. In kuwa Layla ta ƙyalla ido ta gani, na san ranta zai ɓaci sosai! Ka ga in haka ta faru na sami Dauda a hannuna ke nan, kai kuma sai ka bi Layla. Da ma abin da kake so ke nan ko?

**TAFIDA:** Kin ga Maryam, je ki! Akwai wani shiri da nake yi, bai kamata a gan mu tare yanzu muna magana ba. Je ki kawai!

**MAI BA DA LABARI:**

Lokacin da Dauda ya nuna wa Tafida kuros ɗin da yake wuyansa, kawai sai ya ciro masa shi ba tare da ya yi wani tunani ba, saboda aikin gida da aka bayar na lissafi ya sha masa kai. Sai kawai Tafida ya sa shi a aljihu, amma Dauda bai lura ba.

**MAI GABATARWA:**

Wannan shi ne ƙarshen shirin "Ji Ka Karu" na yau. Sai ku biyo mu domin jin yadda shirin na takwas zai kasance a mako mai zuwa. Shin ko Dauda zai faɗa tarkon da Tafida ya kafa masa a cikin shirinmu na gaba a kan "Haɗin Kan Mutanen Sodangi"? Kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraro ko kuma aiko da tsokaci, wato www.dw-world.de/lbe.